# FADAKARWA

## A kan: Kasuwanci da dabarun sai da kaya

## kashi na 6a: Hanyar dabarun saye da sayarwa

### Menene dabarun saye da sayarwa?

Dabarun saye da sayarwa wani muhimmin bangare ne na kasuwanci, wanda ya kunshi:

1. Burin da mutum ya ke so ya cimma a harkokinsa, kamar:
   a. Bunkasar ciniki.
   b. Takaita kashe kudi don tallan kaya.

2. Tsarin yadda za a iya cimma burin da a ka sa a gaba, misali:
   a. Ta hanyar wadata kasuwa da kaya.
   b. Bunkasa tallan kaya.
   c. Kara ingancin kaya.
   d. Samar da kaya a farashi mai sauki.

### Matakan dabarun saye da sayarwa

Lallai ne a lura da wadannan abubuwa wajen neman nasarar harkokin kasuwanci :

### 1. Kyakkyawan nazari a kan yanayin kasuwa, misali a lura da

- Sauran yan kasuwa, me su ke sayarwa, a ina suke, su nawa ne, menene sirrin nasararsu, su wane ne abokan harkokinsu
- Wanne kaya a ka fi bukata?
- Yaya za a samo kayan da za a kawo kasuwa, kuma daga ina, sa'annan a nawa za su zo kasuwa?

Menene matsayinka a kasuwanci: kana da cikakken ilimin kasuwanci., ka iya ciniki, ka iya tsara harkar kasuwanci a rubuce, ka iya tattara muhimman bayanan kasuwa ta hanyar.

- Lura da yanayin kasuwa?
- Tattaunawa da jama'a a kan bukatunsu da gamsuwarsu.?
- Amfanin da zurfin tunani wajen yanke hukunci, mai kyau?

## 2. Neman abokan ciniki

Ya wajaba a nemi abokan ciniki a hankali, a san inda suke, me su ke bukata da kuma karfin aljihunsu.

Za a iya rarraba abokan ciniki aji-aji, misali, manona masara da ban, na shinkafa da ban, ko kuma manoman kauyuka da ban, da ban. Wannan zai taimaka wajen fahimtar tafiyar kasuwa da kuma gamsar da abokan ciniki.

## 3. Tabbatar da samuwar kaya a kasuwa

Bayan an gano abokan ciniki da abubuwan da suke bukata to, lalle ne a tabbata da shigar da kaya kasuwar da aka zaba ko da yaushe. Sabo da haka yana da kyau a san kayan da aka fi bukata a kawanne lokaci, rani da damina.

## 4. Sirri hudu (4) na nasarar kasuwa a takaice

1. Tabbatar da kaya a kasuwa.
2. Samar da kyakkyawan farashi.
3. Tabbataccen matsuguni domin kasuwanci.
4. Tallatar da kaya.

## 5. Canje-canjen yanayin kasuwanci

Ya wajaba a lura da dabarun kasuwanci da kyau da kuma yadda kasuwa kan juya. Lallai ne kuma a kula da yanayin canje-canje a tafiyar kasuwa, ta hanyar yin kyakkyawan nazarin. Idan mutum bai lura da canjin al'amura a kasuwa ba, to wata rana zai kwana a ciki.